**Daga Littattafan Da Ma'aikatar Harkokin Addinin Musulunci, Da Wakafai, Da Kuma Wa'azi Da Shiryarwa Ta Buga**

# Akidar Ahlus~Sunna


Wallafar

Shaikh Muhammad bin Salih Al~Uthaimin

**Da Harshen Hausa**

Tarjamar

**Shaikh Shu'aib Abubakar Umar**



**Offishin Buga Takardu Da Yadasu Na Ma'aikatar Suka Dauki Nauyin Kulawa Da Bugunsa**

**1435 H**

# AKIDAR

**Ahlus -- Sunna**

**wallafar**

**Shaikh Muhammad Salih**

**At-Uthaimin**

**Tarjamar**

**Shaikh Shu'aib Abubakar Umar**

**Da**

**harshen hausa**

**wadanda suka buga suka kuma**

**watsa sune**

**Darul Ifta a Riyadh**

**Mamlakar**

**Larabawa ta Sa'udiyya**

**wakafi ne**

بسم الله الرحمن الرحيم

© وزارة الشؤون الإسلامية والأوقاف والدعوة والإرشاد ، ١٤٢٠ هـ
فهرسة مكتبة الملك فهد الوطنية أثناء النشر.

العثيمين، محمد بن صالح
عقيدة أهل السنة والجماعة .- الرياض.
٧٢ص ، ١٤×٢٠ سم
ردمك ٩٩٦٠-٢٩-٢١٩-٣
(النص باللغة الهوسا )
١-الإيمان (الإسلام) ٢- العقيدة الإسلامية أ- العنوان.
ديوي ٢٤٠ ١٩/٠٤٧١

رقم الإيداع : ١٩/٠٤٧١
ردمك : ٩٩٦٠-٢٩-٢١٩-٣

الطبعة الثانية عشرة
١٤٣٥ هـ

# NA FARA DA SUNAN ALLAH, MAGAMIN JINKAI A DUNIYA

# MAKEBIN JINKAI A LAHIRA

## GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah shi kadai, kuma tsira da aminci su tabbata ga wannan da babu wani Annabi bayansa, da danginsa da kuma sahabbansa.

Bayan haka, hakika na yi nazarin littafin nan da dan uwana babban malami mai suna Sheikh Muhammad bin Salih Al Uthaimin, ya wallafa a kan tsayayyar akida a takaice, kuma na ji duk abinda ya kumsa, sai na same shi ya hade duk wani bayani game da akidan nan ta 'yan sunna da Jama'a, a cikin hanyar tauhidi (kadaita Allah da bauta) da kuma kadaita shi cikin Sunayensa da sifofinsa (wato kada a hada shi da kowa cikinsu). Kamar kuma yanda ya yi bayani game da wajibciyin bangaskiya da mala'iku da littattafai da manzanni, da ba da gaskiya da ranar kiyama, (rayuwa bayan mutuwa).

Ya kuma yi bayani game da wajibcin yarda da kaddara al herinsa da sharrinsa. Ya ma hada wasu zantuttuka masu amfani da dama dangane da akida, wadanda suke da wuya a same su a cikin sauran litattafai da aka wallafa a cikin fannin tauhidi Allah dai ya saka masa da alheri, ya kuma kara masa ilimi da kuma shiriya, ya kuma sa ma wannan

littafi nasa da ma duk sauran littattafai da ya wallafa albarka ya kuma sanya mu tare da shi, da ma duk sauran 'yan uwa cikin shiryayyu, kuma masu shiryarwa, wadanda ke kira zuwa ga hanyar Allah a kan basira lalle Shi Allah sarki ne mai ji kuma kusa yake (Ga mai kiransa).

**SHAIKH ABDUL AZIZ BIN BAZ**

# NA FARA DA SUNAN ALLAH, MAGAMIN JINKAI A DUNIYA

# MAKEBIN JINKAI A LAHIRA

Godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikai, kuma kyakyawan karko yana ga masu kiyaye dokar Allah, kuma babu gaba sai aga azzalumai. Na kuma sheda cewa babu wani abin bauta sai Allah. Shi kadai yake, ba shi da abokin tarayya, bayyanannar Sarauta ta gaskiya ta sa ce. Kuma na sheda cewa lalle Muhammadu bawansa ne kuma Manzonsa ne. Shi ne karshen Annabawa, kuma shi ne shugaban masu kiyaye dokar Allah. Tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi tare da sahabbansa da wadanda suka bi su da kyakyawan aiki, har zuwa ranar kiyama.

Bayan haka, lalle Allah ta'ala ya aiko Manzonsa Muhammadu S.L.A.W.S. da shiriya kuma da addini na gaskiya, don ya zama rahama ga talikai, ya kuma zama abin kwaikwayo ne ga masu aiki (na addini) ya kuma zama hujja ne ma (Allah) a kan bayi baki daya.

Da wannan manzo ne, kuma da littafin nan da aka saukar masa tare da cikakkar hikima, Allah ya bayyana duk wasu abubuwa da za'a iya samun reno na gari a cikinsu da za su zamo dalilin daidaituwar halukan bayi cikin sha'anin duniyarsu da ta lahirarsu; ba za su kuma samu haka ba

face daga ingantattar akida, da kuma daidaita ayyuka da halaye na gari.

Manzon Allah S.L.A.W.S. ya shinfida wa Al'ummarsa farar hanya da ba ta da wani duhu, babu wanda zai baude mata sai hallakakke.

Akan wannan hanya ce duk Al'ummarsa wadanda suka amsa kiran Allah, suka kuma amsa kiran Manzonsa suka bi. Wadanda ake nufi, sune sahabbansa da mabiyansu, tare da wadanda suka bi gurabunsu cikin kyautata aiki, wadannan sune zababbun halittan Allah.

Sun tsaya a kan Shari'ar Ma'aikin Allah suka kuma yi riko da sunnan nan tasa, suka rike ta da kyau da hakoransu, suka bi sunnan nan ta Manzon Allah, S.L.A.W.S. cikin akidarsu, da Ibadarsu, da kuma cikin dabi'arsu da halayensu. Da haka suka zamo jama'a da ba su kauce wa gaskiya. Kuma duk wanda ya kara da su sai ya kai kasa. Wai a nuna masu wani walakanci, ko kuma a saba masu, duk ba su damu ba. Suna tsaye ne a kan haka har sai al'amarin Allah ya zo. Mu kuma muna yi wa Allah godiya cewa muna nan tare da su a kan wannan tafarki nasu. Muna kuma rike da hanyar nan ta su wadda aka cirota daga Al'kur'ani da hadisi, kuma ba mu fadi wannan zance ba face kawai don mu tabbatar da godiyarmu ga ni'imar da Allah yayi mana, kuma don mu nuna wa mutane irin halaye da suka zama wajibi a kan duk muminai su kasance a kai.

Allah Ta'ala muke roko ya tabbatar da dugaduganmu tare da sauran Al'ummar musulmai a kan zance na gaskiya, a cikin dukkan rayuwarmu ta duniya da ta lahira. Muna kuma rokon sa da ya yi mana baiwar jinkai daga gare shi; don kuwa shi ne Sarki mai jinkai.

Saboda muhimmancin abin da wannan littafi ya tara wanda za mu yi zance a kansa da kuma ganin cewa ra'ayin mutane ya sha bambam da abinda wannan littafi ke kunshe da shi kowa da irin nasa zabi da ya dace da tasa zuciyar, sai na so in takaita zance na a cikin wannan littafi kawai a kan akidarmu mu 'yan sunna da Jama'a (Ahlus sunna wal jama'a). Ita akidar tamu kuwa, ita ce ba da gaskiya da Allah da mala'ikunsa, da littattafansa, da manzanninsa, da ranar karshe, da ba da gaskiya da kaddara, (Shine a yarda da duk abinda kaddara ta zo da shi na Alheri da na sharri). Ina kuma dada rokon Allah Ta'ala ya sanya wannan littafi ya zama ya dace da yardarsa, ya kuma zama karbabbe da zai amfani dukkan bayi baki daya.

## AKIDARMU

Akidarmu (kudurcin zucci) itace: ba da gaskiya da Allah, da Mala' ikunsa da littattafansa da manzanninsa, da ranar lahira, da kuma imani da kaddara alherinta ko sharrinta.

Muna ba da gaskiya cewa Allah shine Mahalicci, mai tsara dukkan lamurammu. Kuma duk wani abin bauta banda Allah karya ne.

Muna kuma ba da gaskiya da sunayensa da sifofinsa. Wato abin nufi shine, mun tabbatar cewa Allah Ta'ala yana da wasu sunaye da wasu sifofi kyawawa, cikkaku kuma madaukaka.

Muna kuma ba da gaskiya da kadaituwar Allah cikin duk abin da aka ambata can da farko, cewa shi Allah ba shi da abokin tarayya cikin kasancewarsa Mahalicci abin bauta da gaskiya, kuma ba shi da abokin tarayya a cikin sunayensa, da kuma cikin sifofinsa.

Allah Ta'ala yace.

﴿ رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا فَٱعۡبُدۡهُ وَٱصۡطَبِرۡ لِعِبَٰدَتِهِۦۚ هَلۡ تَعۡلَمُ لَهُۥ سَمِيّٗا ﴾

"Ubangijin sammai da kassai, da abin da ke tsakaninsu. Ka bauta masa, kuma ka daure akan bauta masa, ko ka san wani takwara gare shi." (Maryam:65)

Muna ba da gaskiya cewa shi ne:

﴿ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡحَيُّ ٱلۡقَيُّومُۚ لَا تَأۡخُذُهُۥ سِنَةٞ وَلَا نَوۡمٞۚ لَّهُۥ مَا فِي
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ مَن ذَا ٱلَّذِي يَشۡفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذۡنِهِۦۚ يَعۡلَمُ مَا بَيۡنَ
أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡۖ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَيۡءٖ مِّنۡ عِلۡمِهِۦٓ إِلَّا بِمَا شَآءَۚ وَسِعَ
كُرۡسِيُّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَۖ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفۡظُهُمَاۚ وَهُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡعَظِيمُ ﴾

Allah babu wani abin bauta sai shi, shi ne rayayye (da ba ya mutuwa) mai daidaita lamari. Gyangyadi baya kama shi, balantana bacci. Shine da duk abin da ke cikin sammai da kasa, (halittansa ne, mallakansa ne, kuma bayinsa ne) wane ne yake da ikon ceton (wani) a gunsa ba da izininsa ba; yana sane da abin da ke gabansu da wanda ke bayansu. Kuma babu abinda suka sani game da iliminsa sai wanda ya so (ya nuna masu). Kujerar sarautarsa ta yalwaci sammai da kasa (wato ta fi su girma) kuma kiyaye su bai gagare shi ba (kikaye sama da kasa) shine madaukaki kuma Mai girma.

Muna kuma ba da gaskiya cewa,

Shine Allah wannnan da babu wani abin bautawa sai shi, masanin abinda ya buya da wanda ke sarari. Shi ne magamin jinkai (ga mumunai da kafirai), kuma shine makebin jinkai (ga mumunai kawai a lahira), mai iko da kowa, Buwayayye, mai girma Mabudan gaibi na gunsa, babu wanda ya san su sai shi, yana kuma sane da abin da ke cikin sarari da cikin teku. Babu wani ganye da zai fadi face yana sane da shi, babu wata kwaya a cikin duhun kasa, danya take ko busassa, face (suna) cikin wani bayyanannen littafi.

Muna kuma ba da gaskiya cewa:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥ عِلْمُ ٱلسَّاعَةِ وَيُنَزِّلُ ٱلْغَيْثَ وَيَعْلَمُ مَا فِى ٱلْأَرْحَامِ ۖ وَمَا تَدْرِى نَفْسٌ مَّاذَا تَكْسِبُ غَدًا ۖ وَمَا تَدْرِى نَفْسٌۢ بِأَىِّ أَرْضٍ تَمُوتُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٌۢ ﴾

Sanin (ranar) kiyama na gunsa shi kadai, (shi) kuma ke saukar da hadari,kuma yana sane da abinda ke cikin mahaifa. Kuma babu wata rai da ta san abinda za ta aikata gobe, kuma babu wata rai data san kasar da za ta mutu; lalle Allah masani ne kuma mai labarin komai.

Muna kuma ba da gaskyiya cewa lalle Allah yana magana da abinda ya so (a) lokacin da ya so, yanda (kuma) ya so.

﴿ وَكَلَّمَ ٱللَّهُ مُوسَىٰ تَكۡلِيمًا ﴾

"Allah ya yi magana, da (Annabi) Musa magana ta hakika".

﴿ وَلَمَّا جَآءَ مُوسَىٰ لِمِيقَٰتِنَا وَكَلَّمَهُۥ رَبُّهُۥ ﴾

A yayinda (Annabi) Musa ya zo ma al'kawarinmu, kuma "Uban gijinsa yayi zance dashi"

﴿ وَنَٰدَيۡنَٰهُ مِن جَانِبِ ٱلطُّورِ ٱلۡأَيۡمَنِ وَقَرَّبۡنَٰهُ نَجِيًّا ﴾

"Kuma sai muka yi kiransa daga nan kusa da dutsen nan da ke dama, sai muka kusantar da shi, yana abin ganawa). Muna kuma ba da gaskiya cewa:

﴿وَلَوْ أَنَّمَا فِي الْأَرْضِ مِن شَجَرَةٍ أَقْلَامٌ وَالْبَحْرُ يَمُدُّهُ مِن بَعْدِهِ سَبْعَةُ
أَبْحُرٍ مَّا نَفِدَتْ كَلِمَاتُ اللَّهِ إِنَّ اللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ﴾

In da dai a ce ruwan teku ya kasance taddawa ga zancen ubangijina, da (ruwan) tekun ya kare gabannin zance Ubangiji na ya kare) Ya kuma ce:

﴿قُل لَّوْ كَانَ الْبَحْرُ مِدَادًا لِّكَلِمَاتِ رَبِّي لَنَفِدَ الْبَحْرُ قَبْلَ أَن تَنفَدَ كَلِمَاتُ رَبِّي وَلَوْ
جِئْنَا بِمِثْلِهِ مَدَدًا﴾

Kuma da dai ace duk abin da ke bayan kasa na daga itatuwa su zama al'kalumma, kuma (Ruwan) teku ya zama masu taddawa, a kuma samu wasu irin wannan tekun bakwai su karu a bayansa, zancen Ubangijina ba zai kare ba. Lalle Allah buwayayye ne (kuma) gwani.

Allah ya tsarkaka ga barin abin da suke hada shi da su. Shine Allah mai hallitta. Sammai da kassai suna yi masa tasbihi (suna tsarkake shi) shine Buwayayye kuma gwani).

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle shi ne ke Mallakan Sammai (bakwai) da kasssai (bakwai).

Yana halittan abinda yaso, ya bai wa wanda ya ga dama 'ya'ya mata, ya kuma bai wa wanda ya ga da ma 'ya'ya maza. Ko kuma ya surka masu maza da mata, ya kuma mai da wanda ya ga dama bakararre (wanda ba ya haihuwa.) lalle shi masani ne kuma mai iko.)

Muna kuma ba da gaskiya cewa:

﴿ لَيْسَ كَمِثْلِهِۦ شَىْءٌ ۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ * لَهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ ۚ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴾

Lalle babu wani abu mai kama da shi, shine, mai ji, mai gani. Ragamar sammai da ta kasa nasa ne: ya na shimfida arziki ga wanda ya so, ya kuma kuntata (ma wanda ya so) lalle shi masanin komai ne.)

Muna kuma ba da gaskiya cewa:

﴿ وَمَا مِن دَآبَّةٍ فِى ٱلْأَرْضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزْقُهَا وَيَعْلَمُ مُسْتَقَرَّهَا وَمُسْتَوْدَعَهَا ۚ كُلٌّ فِى كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ﴾

Babu wata dabba, wato mai rarrafe a ban kasa, face arzikinta na ga Allah. Ya san matabbatarta da ma'ajiyarta, duk suna cuna cikin wani bayyanannen litaffi (lauhul mahfuz).

Muna kuma ba da gaskiya cewa: lalle kalmominsa sune mafi cikakkun kalmomi a gaskiya wajen labari da kuma adalci wajen hukunci, kuma mafiya kyau wajen zance. Allah Ta'ala ya ce:

﴿ وَتَمَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ صِدْقًا وَعَدْلًا ﴾

(Kalmar ubangijinka ta cika da gaskiya da adalci).

Ya kuma ce:

﴿وَمَنْ أَصْدَقُ مِنَ اللَّهِ حَدِيثًا﴾

(wanene yafi Allah gaskiyar zance?

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle kur'ani mai girma maganar Allah Ta'ala ne; ko shakka babu. Kuma shine ya jefa shi zuwa ga Mala'ika Jibrilu, sai kuma shi Jibrilu ya saukar da shi ga zuciyar Mà'aikin Allah S.L.A.W.S. Allah Ta'ala yace:

﴿قُلْ نَزَّلَهُ رُوحُ الْقُدُسِ مِن رَّبِّكَ بِالْحَقِّ﴾

Ka ce tsarkakken rai shine ya saukar da shi da gaskiya (wato Jibilu).

Ya kuma ce.

﴿وَإِنَّهُ لَتَنزِيلُ رَبِّ الْعَالَمِينَ * نَزَلَ بِهِ الرُّوحُ الْأَمِينُ * عَلَىٰ قَلْبِكَ لِتَكُونَ مِنَ الْمُنذِرِينَ * بِلِسَانٍ عَرَبِيٍّ مُّبِينٍ﴾

"Lalle abin saukarwa ne (wato Kur'ani) da ga Ubangijin talikai. Amintaccen ran nan ya saukar da shi (wato Jibrilu) a bisa ga zuciyarka, don ka kasance cikin masu gargadi, kuma da harshe ne na larabci wanda yake bayyananne."

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala yana sama ga bayinsa da zatinsa da kuma sifofinsa, don fadinsa da ya yi cewa:

﴿وَهُوَ ٱلْعَلِيُّ ٱلْعَظِيمُ﴾

"Kuma shine madaukaki, mai girma."

Da kuma fadinsa cewa:

﴿وَهُوَ ٱلْقَاهِرُ فَوْقَ عِبَادِهِۦ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ﴾

"Shine mai rinjaya a bisa ga bayinsa, shine gwani masanin komai."

Muna kuma ba da gaskiya, cewa lalle:

﴿إِنَّ رَبَّكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ﴾

Ubangijinku shi ne ya halicci sammai da kasa cikin kwanaki shida, sa'annan ya daidaita a bisa kan Al'arashi, yana juya lamarin bayi.

Abin nufi da daidaituwarsa a kan Al'arashi, shine daukakarsa bisa gare shi da zatinsa daidaita da ta dace da sarautarsa, da kuma girmansa, babu mahluki da ya san hahikaninta sai shi Allah.

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle shi Allah madaukakin sarki, duk da cewa yana sama kan Al'arashi, yana tare da bayinsa, yana kuma sane da halayensu, yana kuma jin zantuttukansu, yana kuma ganin ayyukansu, yana juya lamuransu, yana azurtar da talaka, yana kuma dora wanda ya samu karaya, yana kuma daga kafadun bayinsa, yana bai wa wanda ya ga dama sarauta, ya kuma kwace sarauta daga wanda ya ga dama, alheri hannunsa yake, shi kuma ne ke da iko a kan komai. Duk wanda kuma ya kasance a kan irin wannan Sha'ani, babu shakka yana tare da bayinsa ko da yake yana saman Al'arashinsa.

﴿ لَيْسَ كَمِثْلِهِۦ شَىْءٌ ۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ ﴾

Babu wani abu da ya yi kama da shi (Allah) shi ne mai ji (kuma) mai gani.

Ba za mu fadi irin zancennan da 'yan Hululiyya ko kuma 'yan Jahmiyya da makamantansu ke fadi ba, cewa Allah yana ko ina tare da bayinsa a bayan kasa. Kuma duk wanda ya fadi haka muna gani cewa ya kafirta kuma ya bata, don kuwa ya sifanta Allah da abin da bai kamace shi ba na tauyayyun kamanni.

Muna kuma ba da gaskiya da duk abubuwan da Ma'aikin Allah S.L.W.S. ya fada game da Allah, cewa shi Allah yana sauka zuwa ga saman nan ta duniya ko wane dare har izuwa sulusin dare na karshe, yana cewa: wa zai

kirayeni, in amsa masa? Wa zai roke ni in bashi? Wa zai nemi gafara in gafarta masa?

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle shi Allah mai tsarki kuma da daukaka, zai zo ranar kiyama, don ya yi hukunci tsakanin bayi sabili da fadinsa Ta'ala. A hir! bari wannan maganar, idan aka dandake kasa dandakewa, kuma Ubangijinka ya zo, mala'iku kuma suka yi jere safu safu. Ranar za'a zo da wutar jahannama, rannan ne mutun zai tuna da Allah, tunawar kuma ba za ta yi masa amfani ba.

Muna kuma ba da gaskiya cewa shi Allah Shine mai aikata abin da ya so. Muna kuma ban gaskiya cewa: nufin Allah (abinda ya so) iri biyu ne. Akwai Irada Kasantacciya: Ita ce wacce abin da ya nufa yake afkuwa, ko da kuwa wannan abin bai kasance abin soyuwa ne a gare shi ba. Ita wannan dangi ta irada ita ce ake nufi da mashi'a, wato abin da Allah ya nufi afkuwarsa tun kafin halitta. Kamar yadda Allah Ta'ala ya fada: (In da Allah ya so da ba su yaki juna ba, sai dai shi Allah yana aikata abin da ya so). Ya kuma ce:

﴿إِن كَانَ ٱللَّهُ يُرِيدُ أَن يُغْوِيَكُمْ هُوَ رَبُّكُمْ﴾

(In Allah ya kasance yana nufin ya batar da ku, shi ne Ubangijinku.)

Dangi na biyu, itace Irada Shar'iyya: Ma'anarta abin da Allah ya so, ko da kuwa bai yi nufin afkuwarsa ba.

Kamar fadin Allah Ta'ala da ya yi cewa

﴿وَٱللَّهُ يُرِيدُ أَن يَتُوبَ عَلَيْكُمْ﴾

(Allah yana son ya karbi tubanku).

Muna kuma ba da gaskiya cewa; lalle su wadannan dangogi biyu na Iradar Allah, duk sun rataya ne da hikimar Allah; duk abin da Allah ya hukunta a kan bayinsa tun farkon hallita, ko kuma ya kallafa wa bayinsa na ibadu, duk tare da hikima ce, ko da mun gano hikimar ko ba mu gano ba saboda karancin ilimi da ke tare damu, ko kuma ya zamana hankalin namu ne bai kai fahimtar haka ba. Allah Ta'ala yace:

﴿أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِأَحْكَمِ ٱلْحَٰكِمِينَ﴾

Ashe kuwa Allah ba shi ne fiyayyen masu hikima ba?

Ya kuma ce:

﴿وَمَنْ أَحْسَنُ مِنَ ٱللَّهِ حُكْمًا لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ﴾

wanene ya fi Allah iya hukunci a wurin mutane da suka sakankance (da Allah)

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala yana son waliyyansa, su kuma suna son shi, yace:

﴿ قُلْ إِن كُنتُمْ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحْبِبْكُمُ ٱللَّهُ ﴾

Ka ce; in dai kun kasance kuna son Allah, to ku bi ni, Allah·zai so ku).

Ya kuma ce: da sannu Allah zai zo da wasu mutane yana son su suma suna son shi.

Ya kuma ce:

﴿ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴾

Allah yana son masu hakuri.

Ya kuma ce:

﴿ وَأَقْسِطُوٓا۟ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُقْسِطِينَ ﴾

ku yi adalci, lalle Allah na son masu adalci.

Ya kuma ce:

﴿ وَأَحْسِنُوٓا۟ ۛ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴾

Ku kyautata, lalle Allah na son masu kyautatawa.

Muna kuma ba da gaskiya cewa: lalle Allah Ta'ala ya yarda da duk ayyuka da zantuttuka na ibadu da shi Allah

ya Shar'anta. Yana kuma kin duk abubuwa da ya yi hani ga barin su. Yace:

﴿إِن تَكْفُرُوا فَإِنَّ اللَّهَ غَنِيٌّ عَنكُمْ ۖ وَلَا يَرْضَىٰ لِعِبَادِهِ الْكُفْرَ ۖ وَإِن تَشْكُرُوا يَرْضَهُ لَكُمْ﴾

In kun Kafirta, to lalle Allah ya wadatu ga barin ku, kuma (shi Allah) bai yardar ma bayinsa kafirci ba. Kuma lalle in kun gode (in kun bauta masa) zai yarde maku shi, (ai bautar). Ya kuma ce:

﴿وَلَٰكِن كَرِهَ اللَّهُ انبِعَاثَهُمْ فَثَبَّطَهُمْ وَقِيلَ اقْعُدُوا مَعَ الْقَاعِدِينَ﴾

(Amma sai Allah ya ki fitarsu (zuwa yaki), sai ya zaunar da su, aka ce masu ku zauna tare da masu zama).

Muna kuma ba da gaskiya cewa: lalle Allah Ta'ala yana tabbatar da yardarsa a kan wadannan da suka yi ban gaskiya da Allah, suka kuma yi aiki na gari. Yace:

﴿رَّضِيَ اللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا عَنْهُ ۚ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِيَ رَبَّهُ﴾

Allah ya yarda da su kuma suma sun yarda da abin da Allah ya ba su. Samun haka sai wanda ya ji tsoron Allah.

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala ya na yin fushi da wanda ya cancanci fushinsa a cikin kafirai da makamatansu.Yace:

﴿ٱلظَّآنِّينَ بِٱللَّهِ ظَنَّ ٱلسَّوْءِۚ عَلَيْهِمْ دَآئِرَةُ ٱلسَّوْءِۖ وَغَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ﴾

Masu mummunan zato ga Allah, Mummunan sakamako zai tabbata a kansu, kuma Allah yayi fushsi da su. Ya Kuma ce:

﴿وَلَٰكِن مَّن شَرَحَ بِٱلْكُفْرِ صَدْرًا فَعَلَيْهِمْ غَضَبٌ مِّنَ ٱللَّهِ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ﴾

Amma wanda ya bude zuciyarsa ga kafirci, to fushin Allah ya tabbata a kansa, kuma suna da azaba mai girma.

Muna kuma ban gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala yana da fuska wacce ake sifanta ta da daukaka da girma. Allah Ta'ala yace:

﴿وَيَبْقَىٰ وَجْهُ رَبِّكَ ذُو ٱلْجَلَٰلِ وَٱلْإِكْرَامِ﴾

Fuskan nan ta Ubangijinka mai girma da baiwa ita ce za ta wanzu.

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala yana da hannaye biyu masu baiwa, kuma masu girma. Yace:

﴿بَلْ يَدَاهُ مَبْسُوطَتَانِ يُنفِقُ كَيْفَ يَشَآءُ﴾

Hannayensa biyu dai shinfidaddu suke, yana ciyar wa yadda ya ga dama. Ya kuma ce.

﴿ وَمَا قَدَرُوا۟ ٱللَّهَ حَقَّ قَدْرِهِۦ وَٱلْأَرْضُ جَمِيعًا قَبْضَتُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ وَٱلسَّمَـٰوَٰتُ مَطْوِيَّـٰتٌۢ بِيَمِينِهِۦ ۚ سُبْحَـٰنَهُۥ وَتَعَـٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴾

Basu san darajar Allah, gaskiyar darajarsa ba, kasa baki dayanta tana cikin damkarsa, zai kuma nade sammai da (hannunsa na) dama, tsarki ya tabbata gare shi, kuma ya daukaka ga barin abinnan da suke hada shi (da su).

Muna kuma badagaskiya cewa: lalle Allah Ta'ala yana da idanu biyu na gaskiya, don fadinsa da yayi cewa:

﴿ وَٱصْنَعِ ٱلْفُلْكَ بِأَعْيُنِنَا وَوَحْيِنَا ﴾

Ka kera jirgin ruwa a kan idanunmu, kuma tare da wahayimmu, Manzon Allah S.L.A.W.S. kuma yace:

حجابه النور لو كشفه لأحرقت سبحات وجهه ما انتهى إليه بصره من خلقه.

Shamakinsa haske ne. Da zai bude shi wallahi da hasken fuskarsa ya kone duk abin da ganinsa ya tukegare shi daga halittarsa.

Kuma Ahlus-Sunna sun yi ijma'i a kan cewa: Idanun Allah biyu ne. Kuma zancen nan na Ma'aikin Allah

S.L.A.W.S. ya karfafa wannan maganar. Shine fadinsa da yayi game da Dujal. Sai yace: (lalle mai ido daya ne, Kuma lalle shi Ubangijinnan naku kuwa (wato yana nufin Allah) ba mai ido daya bane). Muna kuma badagaskiya cewa lalle Allah Ta'ala

﴿لَّا تُدْرِكُهُ الْأَبْصَارُ وَهُوَ يُدْرِكُ الْأَبْصَارَ ۖ وَهُوَ اللَّطِيفُ الْخَبِيرُ﴾

(idanu ba sa riskuwar sa, shi ke riske idanu, shine (sarki) Mai saukin lamari (kuma) masanin komai.

Muna kuma ba da gasksiya cewa lalle Muminai za su ga Ubangijinsu ranar kiyama.

﴿وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ نَّاضِرَةٌ ﴿٢٢﴾ إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٌ﴾

Wasu fuskoki a wannan rana za su yi kyau, suna masu dubi zuwa ga Ubangijinsu.

Muna Kuma ba da gasiya cewa lalle Allah Ta'ala ba shi da abin kamantawa, saboda cikakkun sifofinsa.

﴿لَيْسَ كَمِثْلِهِ شَيْءٌ ۖ وَهُوَ السَّمِيعُ الْبَصِيرُ﴾

"Babu wani abu da yayi kama da Allah, shine mai ji (kuma mai gani."

Muna kuma badagaskiya cewa lalle

﴿ لَا تَأْخُذُهُۥ سِنَةٌ وَلَا نَوْمٌ ﴾

"Gyangyadi ba ya kama shi, haka nan bacci." Sabo da shi ne rayayye mai tsaye a kan al'amuran bayinsa.

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle ba ya zaluntar kowa saboda cikakken adalcinsa. Mun kuma yarda cewa lalle ba ya rafkana da abin da bayinsa ke aikatawa, saboda cikakken kulawarsa da kuma cewa iliminsa na kewaye da komai.

Muna kuma ba da gaskiya cewa: lalle babu wani abu da ya ke gagarar sa, cikin sama ne ko kuma a ban kasa, sabo da cikakken iliminsa da kuma ikonsa.

﴿ إِنَّمَآ أَمْرُهُۥٓ إِذَآ أَرَادَ شَيْـًٔا أَن يَقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴾

(lalle yanda lamarinsa yake, in yaso aikata wani abu sai kawai yace kasance sai ko ya kasance).

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle gajiya bata samun sa, haka kuma wahala, saboda cikar karfinsa. (Yana cewa):

﴿ وَلَقَدْ خَلَقْنَا ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ وَمَا مَسَّنَا مِن لُّغُوبٍ ﴾

(Hakika mun halicci; Sammai da kasa da abubuwan da ke tsakaninsu, cikin kwanaki shida. Kuma wata gajiya ba ta shafe mu ba).

Muna kuma ba da gaskiya da duk wasu sunaye ko kuma sifofin da Ubangiji ya tabbatar ma kansa, ko kuma Manzonsa S.L.A.W.S. ya tabbatar masa. Sai dai kuma muna nuna matukar kubutarmu ga barin abubuwan nan masu girma biyu da aka yi mana kashedi da barin su. Sune na farko, wato kamanta Allah. Shine kamar mutum ya tabbatar a cikin zuciyarsa ko ya kuma furta da harshensa cewa ita sifar Allah ta yi kama da sifar halitta.

Na biyu wato shine mutum ya tabbatar a cikin zuciyarsa ko kuma ya fada da harshensa cewa; sifar Allah kaza ce, ko kaza, ma'ana cewa sifar Allah haka take ko haka.

Muna kuma ba da gaskiya, kuma mun yarda da kore duk sifa da Allah Ta'ala ya kore ta ga barin zatinsa, ko kuma wanda Manzonsa S.L.A.W.S.ya kore ta ga barin Allah, don kuwa mun yi Imani cewa, kore wadannan sifofi, zai tabbattar da sifa cikakka ga Allah. Kuma duk wani abu da Allah da Manzonsa suka kyale ba su yi wani bayani a kansa ba, mu ma ba za mu ce komai game da shi ba.

Muna ku ma ganin cewa wajibi ne mu bi wannan tafarki, don kuwa Allah Ta'ala dai ya fi mu sanin kansa, sabo da haka duk abin da ya tabbatar na sifofi ga kansa ko kuma ya kore shi wannan abu tabbatacce ne. Kuma Manzon Allah S.L.A.W.S. shi ne ya fi kowa sanin Ubangiji don

kuwa shi ne yafi kowa gaskiya, kuma ya fi kowa fasaha. Duk abin da muke bukata na cikakken ilimi da gaskiya, za mu same su cikin littafinnan na Allah, da kuma hadisin Annabin nan nasa S.L.A.W.S.

Duk wani abu da muka ambata a cikin wannan littafi, na game da sifofin Ubangiji mai girma da daukaka, ko a dunkule, ko kuma dalla-dalla, mun tabbatar da shi ne ko kuma mun kore shi, duk wani bayani da muka yi mun dogara ne ga Kur'ani da hadisin Manzon Allah S.L.A.W.S., kuma muna bin tafarkin shiryayyun magabatan nan na mu ne.

Kuma muna gani cewa; wajibi ne mu fassara nassin nan na Kurani da hadisan nan na Manzon Allah S.L.A.W.S. a kan zahirin su. Muna fassara shi a kan hakikanin ma'anarsa yadda ya dace da Ubangiji mai girma da daukaka.

Kuma bamu yarda da fassarar nan ta mabarnata, wadannan da ke fassara Kur'ani da hadisi ba ta yadda Ma'aikin Allah ya fassara su ba.

Ba mu kuma yarda da hanyannan, ta masu tozartar da sifofin Allah ba wadannan da ke tozartar da ma'anonin kalmomin Kur'ani ba ta yadda Allah da Manzonsa suka nuna ba. Muna kuma nuna kubutarmu daga tafarkin fassarar nan ta masu ketaran iyaka, sune wadanda ke kamanta Ubangiji da bayinsa, da masu kamanta yadda yake.

Mun kuma sakankance cewa lalle abin nan da ya zo cikin Kur'ani ko hadisin Manzon Allah S.L.A.W.S shine gaskiya. Kuma ba'a samun wani sabani tsakanin su a fuskar fassara. Allah mai girma da daukaka yace:

﴿أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ الْقُرْءَانَ وَلَوْ كَانَ مِنْ عِندِ غَيْرِ اللَّهِ لَوَجَدُوا فِيهِ اخْتِلَٰفًا كَثِيرًا ٨٢﴾

(Shin ba za su yi la'akari da Kur'ani ba, ai in da ya fito gun wanin Allah ne, da an samu sabani da dama a cikin sa).

Lalle samun tangarda a cikin zancen mutun, babu shakka yana tabbatar da karyar wannan zance, Kuma wannan sam ba mai yiwuwa ba ne a same shi a cikin littafin Allah, ko kuma a cikin zancen nan na Ma'aikin nan nasa S.L.A.W.S.

Duk wanda ya yi da'awar cewa, za'a iya samun tangarda tsakanin ayoyin Kur'ani, ko kuma cikin hadisin nan na Manzon Allah S.L.A.W.S. to, ko shakka babu cewa zuciyarsa ta ratse, sai ya hanzarta tuba zuwa ga Allah maza ya dawo daga wannan bata nasa.

Kuma babu wanda zai zaci cewa da akwai sabawa juna cikin ayoyin Kur'ani ko kuma cikin hadisan Manzon Allah, S.L.A.W.S. sai mai karancin ilimi ko kuma mai raunin fahimta, ko kuma shine ya kasa maida hankali sosai cikin zurfin tunani da littafin Allah. Babu abinda ya kamace shi sai kawai ya zare dantse ya nemi ilimi don ya fahimci gaskiya, in ko bai samu fahimta ba, to sai ya koma

ga masaninsa ya fawwala masa lamari don yayi masa bayani ya sa ya dena wannan mummunan zato, sai ya fadi irin kalmarnan da masu zurfin hankali su ke fadi. Sai ya ce:

﴿ءَامَنَّا بِهِۦ كُلٌّ مِّنْ عِندِ رَبِّنَا﴾

Mun ba da gaskiya da shi, duka daga gun Ubangijinmu yake.

Ya iya ganewa cewa, lalle littafin nan na Allah da hadisan nan na Manzonsa S.L.A.W.S. babu sabani a cikin su.

## FASALI NA FARKO

Muna ba da gaskiya da mala'ikun Allah Ta'ala; kuma mun yarda cewa lalle su: bayi ne ababan girmamawa, ba su gabatarsa cikin zance (basu fadin abin da Allah bai sa su ba). Kuma da umarninsa suke aiki.

Allah ne ya halicce su, don su bauta masa, su kuma bi horonsa.

﴿لَا يَسْتَكْبِرُونَ عَنْ عِبَادَتِهِۦ وَلَا يَسْتَحْسِرُونَ ۝١٩ يُسَبِّحُونَ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ لَا يَفْتُرُونَ﴾

"Ba sa girman kai ga barin bautarsa. Kuma basa gajiyawa. Suna tasbihi dare da rana ba sa gajiya."

Allah ne ya tsare su ga barin ganin idon mutane, Allah ya kan bayyanar da su fili ga wasu a cikin bayinsa. Hakika Manzon Allah S.L.A.W.S. ya ga malai'ka Jibrilu a kan surarsa ta asali da Allah ya halicce shi akai, sai ga shi nan ya cike duk sararin sama. Kamar kuma yanda ya taba bayyana ga Nana Maryama (Uwar Annabi Isa) cikin kamanni na mutum, har ta yi zance da shi, shi ma ya yi zance da ita. Ya kuma taba zuwa gun Manzon Allah S.L.A.W.S da surar mutum a yayin da shi Manzon Allah S.L.A.W.S. ke zaune tsakanin sahabbansa, kuma babu wanda ya gane shi tsakanin su (sai shi Manzon Allah kawai). Ya zo ba shi da wata alama ta matafiyi, da farar tufa, kuma da bakin gashi. Sai ya zauna kusa da Manzon Allah S.L.A.W.S. ya jinginar da gwiwarsa biyu ga gwiwowin Manzon Allah S.L.A.W.S. biyu, sai kuma ya dora tafukansa biyu a bisa kan cinyoyinsa biyu, sannan ya yi zance da Manzon Allah S.L.A.W.S. Bayan ya bar gurin sai Manzon Allah S.L.A.W.S. ya ba wa sahabbansa labari cewa Jibrilu ne.

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle Mala'iku suna da ayyuka da aka wakilta su da su.

Akwai mala'ika Jibrilu, shine wanda ke dauke da nauyin saukar da wahayi daga gun Ubangiji zuwa ga wanda ya so ya ba shi manzanci.

Mika'ila ma na cikin su, shine aka wakilta masa nauyin kulawa da sha'anin hadari da tsiro.

Israfilu ma daya ne a cikinsu, shine wanda a ka dora masa nauyin hura kaho yayin da za'ayi tashin duniya, da kuma lokacin da za'a rayar da halitta.

Malai'kan mutuwa shi ma daya ne a cikinsu. Shi ne wanda aka wakilta masa nauyin amsar rai a lokacin mutuwa.

Akwai kuma ma'laika da a ka kallafa masa nauyin kulawa da sha'anin duwarwatsi.

Akwai kuma mala'ika, mai tsaron wuta. Shine Malik akwai kuma mala'ikun da ke kulawa da jinjiri a cikin mahaifa.

Akwai wasu kuma da aka kallafa masu kulawa da sha'anin dan Adam, kuma sune masu rubuta ayyukan bayi, duk dan Adam na da mala'iku biyu. Allah Ta'ala yace:

﴿إِذْ يَتَلَقَّى ٱلْمُتَلَقِّيَانِ عَنِ ٱلْيَمِينِ وَعَنِ ٱلشِّمَالِ قَعِيدٌ ﴿١٧﴾ مَّا يَلْفِظُ مِن قَوْلٍ إِلَّا لَدَيْهِ رَقِيبٌ عَتِيدٌ﴾

"Zamanin da Mala'iku guda biyu masu karbar aiki suke kansa suna zaune a dama da hagu. Ba ya fadar wata magana face mai tsaro yana nan tare da shi).

Wasun kuma an dora masu nauyin tambayar mamaci bayani game da Ubangijinsa, da addinisa, da annabinsa. A nan ne Allah ya ce:

﴿ يُثَبِّتُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱلْقَوْلِ ٱلثَّابِتِ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَفِى ٱلْءَاخِرَةِ ۖ وَيُضِلُّ ٱللَّهُ ٱلظَّـٰلِمِينَ ۚ وَيَفْعَلُ ٱللَّهُ مَا يَشَآءُ ﴾

(Allah ya na tabbatar da wadannan da suka badagaskiya (zai tabbatar da su) a kan datacciyar zance a cikin rayuwarsu ta duniya, da kuma ta lahira, kuma sai Allah ya batar da azalumai, kuma Allah yana aikata abin da yaso).

Akwai kuma wasu mala'ikun da aka kallafa masu nauyin kulawa da sha'anin 'yan aljanna. Allah Ta' ala yace:

﴿ وَٱلْمَلَـٰٓئِكَةُ يَدْخُلُونَ عَلَيْهِم مِّن كُلِّ بَابٍ ﴿٢٣﴾ سَلَـٰمٌ عَلَيْكُم بِمَا صَبَرْتُمْ ۚ فَنِعْمَ عُقْبَى ٱلدَّارِ ﴾

(Zasu rika shiga a gunsu ta kowace kofa (suna fadin) aminci ya tabbata a gare ku, sabo da hakuri da kuka yi, madalla da wannan gida mai karko).

Hakika Manzon Allah S.L.A.W.S. ya ba da labari cewa lalle akwai wani daki a cikin sama mai suna Baitul ma'

amur da mala'iku dubu saba'in kan shiga a cikin sa kowace rana. In kuma sun fice, ba su kara dawowa.

## FASALI NA BIYU

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala ya saukar da wasu littattafai ga Manzanninsa, don su zama hujja ne ga talikai. Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala ya saukar da littattaffai tare da kowane Manzo. Dalili kuwa shine fadinsa da yayi cewa:

﴿لَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا بِالْبَيِّنَٰتِ وَأَنزَلْنَا مَعَهُمُ الْكِتَٰبَ وَالْمِيزَانَ
لِيَقُومَ النَّاسُ بِالْقِسْطِ﴾

Hakika mun aiko manzanninmu da hujjoji bayyannu. Muka kuma saukar da littafi da ma'auni (na shari'a) tare da su, don mutane su tsayar da adalci).

Mun san daga cikin wadannan littattafai:

(a) Attaura, shi ne littafin nan da Allah Ta'ala ya saukar wa Annabi Musa, A.S. shine mafi girman littafin Bani Isra'ila. Allah Ta'ala yace:

﴿فِيهَا هُدًى وَنُورٌ يَحْكُمُ بِهَا النَّبِيُّونَ الَّذِينَ أَسْلَمُوا لِلَّذِينَ هَادُوا
وَالرَّبَّٰنِيُّونَ وَالْأَحْبَارُ بِمَا اسْتُحْفِظُوا مِن كِتَٰبِ اللَّهِ وَكَانُوا عَلَيْهِ
شُهَدَاءَ﴾

Akwai shiriya da haske a cikin sa, da shi ne Annabawa (na) Bani Isra'ila wadanda suka mika wiya suke yin hukunci ga, wadannan da suka bi yahudanci, da malamansu da fakihansu, saboda an kiyayar da su littafin (kar su sake shi), kuma sun kasance shaidu a kansa (cewa gaskiya ne).

(b) Injila: shine littafin nan da aka saukar wa Annabi Isa, A.S. Shi kuwa (Injilan) ya zo ne don ya gaskata attaura kuma ya cika ta. Allah Ta'ala yace.

﴿ وَءَاتَيْنَٰهُ ٱلْإِنجِيلَ فِيهِ هُدًى وَنُورٌ وَمُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَهُدًى
وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴾

Kuma muka ba shi injila; da akwai Shriya a cikinsa da haske, kuma mai gaskata abin da ke gaba gare shi ne daga Attaura kuma shiriya ce kuma gargadi ne ga masu kiyaye sabon Allah). Allah Ta,ala kuma yace:

﴿ وَلِأُحِلَّ لَكُم بَعْضَ ٱلَّذِى حُرِّمَ عَلَيْكُمْ ﴾

Kuma don na halatta maku sashi (a cikin) abin da aka haramta maku).

(C) Zabura: itace littafin da Allah Ta'ala ya ba wa Annabi Dauda A.S

(D) Takardun Annabi Ibrahima da Annabi Musa, amincin Allah ya tabbata, a gare su (su biyu).

(E) Alkur'ani mai girma, shi ne littafin da Allah Ta'ala ya saukar da shi ga Annabinsa Muhammad cikamakin Annabawa. Allah yace.

﴿ هُدًى لِّلنَّاسِ وَبَيِّنَٰتٍ مِّنَ ٱلْهُدَىٰ وَٱلْفُرْقَانِ ﴾

Shiriya ne ga mutane, kuma bayani ne (da ya fito) cikin shiriya; kuma yana rarrabe (tsakanin gaskiya da karya) (wato shi Kurani)

Ya kasance "mai gaskata abin da ke gaba gareshi, na littafi kuma mai shaida a kansa". Kuma shine littafin da Allah, ya kiyaye shi ga barin wargin masu wargi, da rudanin nan na wadanda suka karkata. Allah yace:

﴿ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا ٱلذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ﴾

(Mune muka saukar da Al Kur'ani, kuma mune zamu kikaye shi).

Don haka shi Kur'ani, zai tabbata hujja ne a kan dukkan mutane har izuwa ranar kiyama. Duk sauran littattafai da suka gabata an iyakance su ne da lokaci na musamman, amfanin su ya kan tuke da zaran an saukar da wani littafin. Kur'ani ya yi bayani matuka game da abubuwa da suke cikin wadannan littattafai na game da jirkita su. Sabo da

haka ba'a lamunce masu rashin jirkita ba. Lalle kuwa an samu yawan jirkita da juya kalmoni daga mahallinsu. Kamar yadda aka samu kurakurai da tawaya da dama a cikinsu.

Allah Ta'ala yace:

﴿ مِّنَ ٱلَّذِينَ هَادُوا۟ يُحَرِّفُونَ ٱلْكَلِمَ عَن مَّوَاضِعِهِۦ ﴾

"Wasu a cikin wadanan da suka bi yahudanci, suna Musanya zance ga barin asalinsa. Ya kuma ce:

﴿ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ يَكْتُبُونَ ٱلْكِتَـٰبَ بِأَيْدِيهِمْ ثُمَّ يَقُولُونَ هَـٰذَا مِنْ عِندِ ٱللَّهِ لِيَشْتَرُوا۟ بِهِۦ ثَمَنًا قَلِيلًا ۖ فَوَيْلٌ لَّهُم مِّمَّا كَتَبَتْ أَيْدِيهِمْ وَوَيْلٌ لَّهُم مِّمَّا يَكْسِبُونَ ﴾

(Azaba ta tabbata ga wadannan da ke rubuta littafi da hunnunsu, sa'annan sai su ce wannan daga Allah (ya ke) don su musanya shi da dan kudi kadan, kaitonsu daga abinnan da suka rubuta, (da hannunsu): kuma kaitonsu daga abinda suke tsuwaurwuta).

Ya kuma ce:

﴿ قُلْ مَنْ أَنزَلَ ٱلْكِتَـٰبَ ٱلَّذِى جَآءَ بِهِۦ مُوسَىٰ نُورًا وَهُدًى لِّلنَّاسِ ۖ تَجْعَلُونَهُۥ قَرَاطِيسَ تُبْدُونَهَا وَتُخْفُونَ كَثِيرًا ﴾

"Ka ce wanene ya saukar da littafin nan da Musa ya zo da shi, wanda ya kasance haskene da shiriya ga mutane? Sai kuka maida shi takarda, kuna bayyanar da sashi, kuna kuma boye mafi yawa). Allah kuma yace:

﴿وَإِنَّ مِنْهُمْ لَفَرِيقًا يَلْوُۥنَ أَلْسِنَتَهُم بِٱلْكِتَٰبِ لِتَحْسَبُوهُ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ
وَمَا هُوَ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ وَيَقُولُونَ هُوَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ وَمَا هُوَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ
وَيَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿٧٨﴾ مَا كَانَ لِبَشَرٍ أَن يُؤْتِيَهُ ٱللَّهُ
ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحُكْمَ وَٱلنُّبُوَّةَ ثُمَّ يَقُولَ لِلنَّاسِ كُونُوا۟ عِبَادًا لِّى مِن دُونِ
ٱللَّهِ﴾

(Lalle wallahi da wasu jama'a cikin su (Bani Isra'ila) da sukan musanya maganar Allah da harshensu, don kuyi tsammanin sa cewa daga littafin yake, shi kuwa ba daga littafin yake ba, suna kuma fadi cewa daga Allah yake, (alhali kuwa) ba daga Allah yake ba, suna yi wa Allah karya a kan sun sani (cewa Karya su ke). Bai kamata ga mutum ba (wanda) Allah ya ba shi littafi, da hukumci da annabci, sa'annan kuma yace wa mutane, ku zamo bayi na koma bayan Allah.) Kuma yace:

﴿يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ قَدْ جَآءَكُمْ رَسُولُنَا يُبَيِّنُ لَكُمْ كَثِيرًا
مِّمَّا كُنتُمْ تُخْفُونَ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ﴾

Ya ku mazowa littafi, hakika Manzonmu ya zo maku, yana yi maku bayanin mafi yawaicin abin da kuka kasance kuna boyewa daga littafi (Attaura da Injila). Har zuwa inda Allah Ta'ala ke fadi cewa:

﴿لَقَدْ كَفَرَ الَّذِينَ قَالُوٓا إِنَّ اللَّهَ هُوَ الْمَسِيحُ ابْنُ مَرْيَمَ﴾

(Hakika, wadannan da suka ce Isa dan Maryama shine Allah sun Kafirta.

## FASALI NA UKU

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala ya aiko da manzanni zuwa ga halittarsa, Yace:

﴿رُّسُلًا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى اللَّهِ حُجَّةٌۢ بَعْدَ الرُّسُلِ وَكَانَ اللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا﴾

Manzanni Masu ba da bushara; kuma masu tsoratarwa; domin kada mutane su samu wata hujja kan Allah (wato kada su samu wani abin fadi game da Allah) bayan (zuwan) wadannan manzanni, Allah ya kasance (sarki ne) buwayayye kuma gwani.

Muna kuma ba da gaskiya cewa: na farkonsu shi ne Annabi Nuhu Na karshen su shi ne Muhammad tsira da

amincin Allah su tabbata a gare shi tare, da sauran Annabawa baki daya. Allah Ta'ala yace:

﴿إِنَّآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ كَمَآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ نُوحٖ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ مِنۢ بَعۡدِهِۦۚ﴾

(Mu mun yi wahayi zuwa gareka kamar yadda muka yi wahayi zuwa ga Nuhu, da annabawa da suka zo bayansa). Ya kuma ce:

﴿مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٖ مِّن رِّجَالِكُمۡ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَۗ﴾

(Muhammad ba uban daya ba ne daga mazajenku, shi dai Manzo ne na Allah, kuma cikamakin Annabawa).

Kuma lalle fiyayyensu shi ne Muhammad sa'annan Ibrahima, sa'annan Musa, sa'annan Nuhu, Sa'annan Isa dan maryama, kuma wadannan sune abin nufi cikin Kurani, inda Allah Ta'ala ke fadi cewa:

﴿وَإِذۡ أَخَذۡنَا مِنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِيثَٰقَهُمۡ وَمِنكَ وَمِن نُّوحٖ وَإِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَى ٱبۡنِ مَرۡيَمَۖ وَأَخَذۡنَا مِنۡهُم مِّيثَٰقًا غَلِيظٗا﴾

(Ka tuna) yayin da muka riki Al-kawari daga Annabawa, kuma daga gunka (wato Annabi Muhammadu) daga kuma Nuhu, da Ibrahima, da Musa, da Isa dan Maryama, mun riki Alkawari mai kauri daga gare su.

Mun kuma kudurta cewa lalle shari'o'innan na Manzon Allah, S.L.A.W.S. tafi duk sauran shari'oi'in wadannan manzanni, don fadin Allah Ta'ala da yayi cewa:

﴿ شَرَعَ لَكُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا وَصَّىٰ بِهِۦ نُوحًا وَٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ وَمَا وَصَّيْنَا بِهِۦٓ إِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَىٰٓ أَنْ أَقِيمُوا۟ ٱلدِّينَ وَلَا تَتَفَرَّقُوا۟ فِيهِ ﴾

(Allah) ya shar'anta maku game da addini, abin nan da ya hori Nuhu da shi, da kuma abinnan da muka yi maka wahayin sa, da kuma wannan da muka hori Ibrahima, da Musa da Isa, cewa ku tsayar da addini kada ku rarrabu.

Muna kuma badagaskiya cewa: lalle dukan manzanni, mutane ne abin halitta, ba su da wata sifa da ta kebantu ga Allah. Allah Ta'ala yace game da sha'anin Nuhu wanda yake shine farkon manzanni:

﴿ وَلَآ أَقُولُ لَكُمْ عِندِى خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ أَعْلَمُ ٱلْغَيْبَ وَلَآ أَقُولُ إِنِّى مَلَكٌ ﴾

Ba nace maku taskar Allah na gu na, Kuma ban san gaibu ba, kuma ba ni ce muku ni Mala'ika ne)

Kuma Allah Ta'ala ya hori Annabinsa wanda shine ya zama karshensu, da ya ce:

﴿قُل لَّآ أَمۡلِكُ لِنَفۡسِى نَفۡعًا وَلَا ضَرًّا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۚ﴾

(Ka ce: Ba na mallaka ma kai na wani amfani, ko kuma cuta face abin da Allah ya so. Kuma ya ce:

﴿قُلۡ إِنِّى لَآ أَمۡلِكُ لَكُمۡ ضَرًّا وَلَا رَشَدًا ﴿٢١﴾ قُلۡ إِنِّى لَن يُجِيرَنِى مِنَ ٱللَّهِ أَحَدٌ وَلَنۡ أَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلۡتَحَدًا﴾

(Ka ce: Ni ba na mallaka muku wata cuta ko wata shiriya. Ka ce ni babu wanda zai iya tsare ni (ga barin azabar Allah) kuma ba ni da wata mafaka koma bayan Allah).

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle su wadannan manzanni suna cikin bayin Allah da Allah ya karrama su da manzanci, ya kuma sifanta su da siffar bauta wacce take ita ce mafi girmar siffa a gun Allah.

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡفُرُونَ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ﴾

(Lalle wadannan da suka kafirce ma Allah da kuma manzanninsa, kuma suna neman raba tsakanin Allah da manzanninsa, kuma suna fadin (cewa) mun ba da gaskiya da sashi (wato na manzannin), mun kuma kafirce ma sashi. Suna so su riki wani tafarki tsakanin wannan. Wadannan sune kafirai na gaske, mu kuma mun yi tattalin walakantacciyar azaba ga kafirai).

Muna kuma ba da gaskiya cewa lalle babu wani Annabi bayan Muhammadu S.L.A.W.S. Kuma duk wanda ya yi da'awar Annabci (ya kira kansa annabi) ko kuma ya gaskata wanda yayi da'awar annabci, lalle ya kafirta. Don kuwa ya karyata Allah da Manzonsa, da kuma duk al'ummar musulmai.

Muna kuma ba da gaskiya cewa: lalle Annabi S.L.A.W.S. yana da hatifofi (Khulafa'u al'rashidun) sune suka maye masa cikin kulawa da Sha'anin al'ummarsa, ta fuskar bada ilimi, da kira zuwa ga addini, da kuma ta fuskar jibintar lamarinsu. Kuma lalle fiyayyensu shi ne Sayyadi Abubakar, shi ne kuma ya fi cancanta da hilafa. Na biyunsu ne Sayyadi Umaru dan Khattab, sa'annan Uthman dan Affan, sa'annan Sayyadi Ali dan Abi dalib, yardar Allah ta tabbata gare su baki daya.

Muna kuma ba da gaskiya cewa, ita wannan al'umma ta Manzon Allah, itace fiyayyar al'umma. kuma ta fi kowace al'umma alfarma a wurin Allah. Dalili kuwa shine fadin Allah madaukakin sarki da yayi cewa:

﴿كُنتُمْ خَيْرَ أُمَّةٍ أُخْرِجَتْ لِلنَّاسِ تَأْمُرُونَ بِالْمَعْرُوفِ وَتَنْهَوْنَ عَنِ الْمُنكَرِ وَتُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ﴾

(Kun kasance kune fiyayyun al'umma da aka fitar ga mutane. Kuna horo da yin nagarta (aikin kirki) kuna kuma

hani ga barin (aikata) mugun aiki, kuma kuna ba da gaskiya da Allah.

Muna kuma ba da gaskiya cewa fiyayyun wannan al'umma ta Manzon Allah S.LA.W.S. sune sahabbai, sa'annan mabiyansu, da kuma mabiyan wadannan.

Kamar kuma yanda muke ba da gaskiya cewa har a nade duniya ba za'a rabu da samun wasu jama'a a cikin wannan al'umma, da za su tsaya a kan gaskiya, kuma sune masu samun nasara, suna tsaye kan haka ne har Allah ya huku nta lamarinsa.

Mun kuma yarda cewa lalle duk wata tarzoma, ko kuma fitina da ta gudana tsakanin sahabban Manzon Allah yardar Allah ta tabbata a gare su, hakika ta auku ne bisa fahimtar kowane daya daga cikinsu, da kuma kokarinsa a cikin bincike. Wanda Allah ya sa ya dace tsakaninsu, babu shakka yana da lada biyu wanda kuma bai dace ba to yana da lada daya, kuma an gafarta masa kuskurensa. Allah yace:

﴿لَا يَسْتَوِي مِنكُم مَّنْ أَنفَقَ مِن قَبْلِ الْفَتْحِ وَقَاتَلَ﴾

(Wadanda suka ciyar (da dukiyarsu) gabannin bude (Makka) suka kuma yi yaki, ba za su zama daya ba (da wadando basu yi haka). Wadannan sun fi girma da daraja da wadannan da suka ciyar bayan bude (Makka), suka

kuma yi yaki, amma kuma kowanne a cikin su, Allah ya yi masa alkawarin Aljanna.) Ya kuma ce:

﴿وَٱلَّذِينَ جَآءُو مِنۢ بَعْدِهِمْ يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱغْفِرْ لَنَا وَلِإِخْوَٰنِنَا
ٱلَّذِينَ سَبَقُونَا بِٱلْإِيمَـٰنِ وَلَا تَجْعَلْ فِى قُلُوبِنَا غِلًّا لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ رَبَّنَآ إِنَّكَ
رَءُوفٌ رَّحِيمٌ﴾

Wadannan kuma da suka zo bayansu, suna fadi, ya Ubangijimmu! Ka gafarta mana (kuma ka gafarta) ma yan uwanmu, wadannan da suka gabace mu da imani; Kuma kar ka sanya wani kunci a cikin zukatammu ga wadannan da suka yi imani, Ya Ubangijimu lalle kai ne mai gafara (kuma) mai jinkai.

## FASALI NA HUDU

Muna kuma badagaskiya da ranar karshe, shine wato ranar kiyama, ranan nan da ba za'a kara samun wata rana a bayanta ba. Ita ce ranar da za'a raya mutane don su wanzu har abada, imma cikin gidan ni'ima, ko kuma cikin gidan azaba mai tsanani. Sabili da haka mun yi imani da rayuwa bayan mutuwa, da Allah Ta'ala zai yi wa mamata, a yayin da Israfilu zai busa kaho busa na biyu. Allah ya ce:

﴿وَنُفِخَ فِي الصُّورِ فَصَعِقَ مَن فِي السَّمَاوَاتِ وَمَن فِي الْأَرْضِ إِلَّا مَن شَاءَ اللَّهُ ۖ
ثُمَّ نُفِخَ فِيهِ أُخْرَىٰ فَإِذَا هُمْ قِيَامٌ يَنظُرُونَ﴾

(sai aka busa kaho, sai wadanda ke cikin sammai (bakwai) da na kasa su mace, Sa'annan kuma aka busa na biyu sai ga su nan tsaye suna duban abinda za a aika ta dasu). Sai mutane su tashi daga kabari zuwa ga Ubangiji, ba su da kaciya, babu wanda ke sanye da takalmi, ballantana riga ko wando, ga su nan tsirara haihuwar uwarsu, ko kaciya ba su da ita).

﴿كَمَا بَدَأْنَا أَوَّلَ خَلْقٍ نُّعِيدُهُ ۚ وَعْدًا عَلَيْنَا ۚ إِنَّا كُنَّا فَاعِلِينَ﴾

(Kamar yanda muka samar da su a farko, haka za mu kuma mayar da su, alkawari ne a kammu mun kasance mu masu aikatawa ne). Muna kuma imani da littattafai na ayyukan mutane, da za'a basu a hannun damarsu ko kuma hannun hagunsu. Allah Ta'ala yace:

﴿فَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَابَهُ بِيَمِينِهِ * فَسَوْفَ يُحَاسَبُ حِسَابًا يَسِيرًا * وَيَنقَلِبُ إِلَىٰ أَهْلِهِ
مَسْرُورًا * وَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَابَهُ وَرَاءَ ظَهْرِهِ * فَسَوْفَ يَدْعُو ثُبُورًا * وَيَصْلَىٰ سَعِيرًا﴾

Amma ka ga wanda aka ba shi littafinsa a hannun damansa, da sannu za ayi masa hisabi mai sauki, kuma zai

koma gun iyalinsa yana mai farin ciki. Amma kaga wanda za'a ba shi littafinsa a hannun hagunsa, da sannu zai yi kiran halaka, kuma zai shiga (wutan sa'ira). Allah kuma ya ce:

﴿ وَكُلَّ إِنسَٰنٍ أَلْزَمْنَٰهُ طَٰٓئِرَهُۥ فِى عُنُقِهِۦ ۖ وَنُخْرِجُ لَهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ كِتَٰبًا يَلْقَىٰهُ مَنشُورًا
ٱقْرَأْ كِتَٰبَكَ كَفَىٰ بِنَفْسِكَ ٱلْيَوْمَ عَلَيْكَ حَسِيبًا ﴾

(kowane mutum za mu lizimta masa takarda (aikinsa) a wuyansa, kuma za mu fitar masa da littafi abude (za mu kuma ce masa) ka karanta littafinka, yau kai da kanka ka isa ka yi ma kanka hisabi).

Muna kuma badagaskiya da ma'auni da za'a ajiye shi ranar kiyama, ba'a zaluntar wata rai ko kadan.

﴿ فَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ خَيْرًا يَرَهُۥ * وَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ شَرًّا يَرَهُۥ ﴾

(Wanda ya aikata aiki na alheri, kwatancin kwayar komayya zai gani, kuma wanda ya aikata mugun aiki kwatancin kwayar komayya zai gani) Allah, ta'ala kuma yace:

﴿ فَمَن ثَقُلَتْ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ * وَمَنْ خَفَّتْ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ
خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ فِى جَهَنَّمَ خَٰلِدُونَ * تَلْفَحُ وُجُوهَهُمُ ٱلنَّارُ وَهُمْ فِيهَا كَٰلِحُونَ ﴾

(Wanda ma'auninsa ya yi nauyi, wadannan sune wadanda suka rabauta, wanda kuma ma'auninsa ya yi rauni wadannan sune wadanda suka yi wa kansu hasara, cikin jahannama za su dawwama.Wuta zata rika kunar fuskarsu (za ka same su) suna masu dame fuska a cikin wannan wuta.

Ya kumace:

﴿مَن جَآءَ بِٱلْحَسَنَةِ فَلَهُۥ عَشْرُ أَمْثَالِهَا ۖ وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَلَا يُجْزَىٰٓ إِلَّا مِثْلَهَا
وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ﴾

(Wanda yazo (lahira) da aiki (daya) mai kyau zai samu irinsa goma, kuma wanda ya zo da mummuman aiki, ba za'a saka masa ba face da kwatamkwacinsa, kuma ba za'a zalunce su ba).

Muna kuma ba da gaskiya da babban ceton nan da Allah ya kebance shi ga Manzon Allah S.L.A.W.S. Zai yi wannan ceton ne da yardar Allah, kuma da izininsa, a yayin da duk mutane za su kasance a cikin bacin rai da bakin ciki, suna kuma cikin halin kaka nikayi. Sai duk mutane su tashi zuwa ga Annabi Adama. Sannan kuma su je gun Annabi Nuhu sannan gun Annabi Ibrahima, sa'annan kuma sai gun Annabi Musa sa'annan Annabi Isa, a karshe sai su je gun Manzon Allah S.L.A.W.S. Duk dai wai suna neman su cece su ne gun Allah daga azabar nan ta wannan fili.

Muna kuma ba da gaskiya da ceton da Allah zai bai wa Manzonsa Muhammad S.L.A.W.S shi da wasu jama'a ta Annabawa, da wasu jama'a ta muminai, da wasu mala'ikun Allah. Za su ceci wasu mu'minai da za'a saka su a wuta.

Kuma lalle Allah Ta'ala zai fidda wasu jama'an muminai daga wuta bada wani ceto ba, wato dai jinkai ne kawai daga gunsa da kuma falalarsa.

Muna ba da gaskiya da tabkin nan na Manzon Allah S.LW.S. Ruwan wannan tabki ya fi nono fari kuma ya fi zuma dadi, kuma kanshinsa wa ne miski. Tsawon wannan tabki ya kai nisan tafiyar wata daya, haka kuma fadinsa. Yawan modarsa kuma wa ne taurarun sama, ga kyau ga yawa. Mu'minai Al'Ummar Manzon Allah za su sha ruwan wannan tabki, kuma duk wanda ya sha wannan ruwa, shi da kishin ruwa dai sun rabu ke nan.

Mun kuma yi imani da siradi da ke shimfide a kan wutar jahannama, wanda a kansa ne kowa zai ketare. Kowane daya kuma zai ketare ne gwargwadon karfin aikinsa da kuma imaninsa.

Farkon wanda zai fara ketara, za'a gan shi ne kamar walkiya, wani kuma zai ketare ne kamar iska, wani kuwa ka rantse da Allah cewa tsuntsune, wani kuma kamar gudun ingarman doki. Manzon Allah S.L.A.W.S. yana tsaye a kan siradi, yana cewa (Allah ka kiyaye Allah ka kiyaye). Ana nan ana cikin ketara, har ketarewar ta kai ga

wadanda ayyukansu na kirki ba sa iya keterar da su siradi a tsaye,sai su koma a rarrafe. A can gefe daya kuma na siradi za ka tadda wasu kugiyoyi a rataye, suna kame duk wanda aka umurce su da kamewa. Akwai wanda za'a kekkece shi ya tsira da kyar, akwai kuma wanda zai abka cikin wuta.

Muna kuma imani da duk abin da ya zo cikin Al-Kur'ani, da hadisin Manzon Allah S.L.A.W.S. dangane da laḅaran wannan rana (wato kiyama) wato tashin hankalinta. Allah daiya yi mana tsari.

Muna kuma ba da gaskiya da Aljanna da kuma wuta, mun yi imani cewa ita Aljanna gida ce ta ni'ima da Allah Ta'ala ya yi tattalinta ga bayinsa muminai masu tsoronsa. A cikin Aljannan, akwai abinda ido bai taba gani ba, kuma kunne bai taba ji ba, kuma bai taba darsuwa a zuciyar wani dan Adam ba. Allah sarkin yace:

﴿ فَلَا تَعْلَمُ نَفْسٌ مَّا أُخْفِيَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعْيُنٍ جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴾

(Babu wata rai da ta san abinda aka boye masu na abubuwa masu sanyaya idanu, wannan, sakamako ne na a binda suka kasance suna aikatawa).

Wuta kuma gida ce ta azaba, da Allah Ta'ala ya yi tattalinta ga kafirai, da suka zalunci kawunansu. Akwai mummunar azaba da ba ta taba sauka a cikin hankali ba ko da rana daya: Allah mai girma da daukaka ya ce:

﴿إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا أَحَاطَ بِهِمۡ سُرَادِقُهَاۚ وَإِن يَسۡتَغِيثُواْ يُغَاثُواْ بِمَآءٖ
كَٱلۡمُهۡلِ يَشۡوِي ٱلۡوُجُوهَۚ بِئۡسَ ٱلشَّرَابُ وَسَآءَتۡ مُرۡتَفَقًا﴾

Mu, Mun yi ma azzalumai tattalin wuta shingen wannan wuta ta kewaye su. In suka nemi agaji (wato neman a shayar da su)sai a agajesu da wani ruwa kamar surkani (ruwan kurji) yana gasa fuska. Tir da wannan abin sha, kuma ta yi muni ta zama mahuta.)

Kuma a halin yanzu aljanna da wuta, suna nan kuma ba za su kare ba har abada. Allah yace:

﴿وَمَن يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ وَيَعۡمَلۡ صَٰلِحٗا يُدۡخِلۡهُ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ
فِيهَآ أَبَدٗاۖ قَدۡ أَحۡسَنَ ٱللَّهُ لَهُۥ رِزۡقًا﴾

(Wanda yayi bangaskiya ga Allah, ya kuma aikata aiki na gari (Allah zai) saka shi Al'janna koramai na gudu karkashinta, zasu dawwama cikin har a'bada. Hakikan Allah ya kyautata masa arziki). Ya kuma ce:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ لَعَنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ وَأَعَدَّ لَهُمۡ سَعِيرًا ﴿٦٤﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ لَّا يَجِدُونَ وَلِيّٗا
وَلَا نَصِيرٗا ﴿٦٥﴾ يَوۡمَ تُقَلَّبُ وُجُوهُهُمۡ فِي ٱلنَّارِ يَقُولُونَ يَٰلَيۡتَنَآ أَطَعۡنَا ٱللَّهَ وَأَطَعۡنَا
ٱلرَّسُولَا﴾

Lalle Allah ya la'anci kafirai, ya kuma yi masu tattalin wutan sa'ira. Za su dawwama a cikinta har abada, ba za su samu wani majibinci ba, ko kuma wani mataimaki. Ranar da za'a rika juya fuskokinsu cikin wuta, sai su rika fadi (cewa) da dai mun sani da mun bi Allah mun kuma bi Manzo).

Kuma duk wanda Kur'ani da hadisi su ka yi masa sheda da shiga Aljana, muna yi masa sheda, ko da kuwa siffarsa kawai aka ambata, ko kuma an ambace shi ne da ainihinsa.

Ma'anar sheda da ainihi, shine sheda da Manzon Allah S.L.A.W.S ya yi wa Sayyadi Abubakar da Umar da Uthmanu da kuma Sayyadi Ali da makamantasu, cewa su 'yan aljanna ne.

Ma'nar yi wa mutum sheda da suffantawa kuma, shi ne sheda da za'ayi wa duk kafiri, ko wani babban mushriki, ko kuma manafuki.

Muna kuma imani da afkuwar fitinar kabari, shi ne wato tambaya da za'a yi wa mamaci a cikin kabarinsa. Za'a yi masa tambaya game da ubangijinsa, da addininsa, da kuma manzonsa. Allah mai girma da daukaka yace:

﴿ يُثَبِّتُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱلْقَوْلِ ٱلثَّابِتِ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَفِي ٱلْءَاخِرَةِ ﴾

(Allah zai tabbatar da wadanan da suka yi imani kan tabatacen zance), (itace kalman nan ta la'ilaha illallahu), a cikin rayuwarsu ta duniya, da ta lahira). Mumini zai samu ikon ba da jawabi, sai ya ce: Allah ne ubangijina, musulunci ne addini na, Muhammadu ne Annabi na.

Amma kafiri, zai ce: ban sani ba, na dai ji mutane na fadin wani zance sai ni ma na fada.

Muna kuma ba da gaskiya cewa mumini yana tare da ni'ima a cikin Kabarinsa. Allah Ta'ala yace:

﴿ٱلَّذِينَ تَتَوَفَّىٰهُمُ ٱلْمَلَـٰٓئِكَةُ طَيِّبِينَ يَقُولُونَ سَلَـٰمٌ عَلَيْكُمُ ٱدْخُلُوا۟ ٱلْجَنَّةَ بِمَا
كُنتُمْ تَعْمَلُونَ﴾

(Wadannan da mala'iku ke amsar rayukansu, suna mutanen kirki, (mala'iku za su ce masu) aminci ya tabbata a gare ku, ku shiga Al'janna don abin da kuka kasance kuna aikata wa).

Muna kuma ba da gaskiya cewa akwai azabar kabari ga wadanda suke azzalumai kuma kafirai. Allah Ta'ala yace:

﴿وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّـٰلِمُونَ فِى غَمَرَٰتِ ٱلْمَوْتِ وَٱلْمَلَـٰٓئِكَةُ بَاسِطُوٓا۟ أَيْدِيهِمْ
أَخْرِجُوٓا۟ أَنفُسَكُمُ ٱلْيَوْمَ تُجْزَوْنَ عَذَابَ ٱلْهُونِ بِمَا كُنتُمْ تَقُولُونَ عَلَى
ٱللَّهِ غَيْرَ ٱلْحَقِّ وَكُنتُمْ عَنْ ءَايَـٰتِهِۦ تَسْتَكْبِرُونَ﴾

(Da dai za ka ga yayin da azzaluman nan ke cikin magagin mutawa, malaiku kuma na shimfida hannuwansu (suna fadin) ku fidda rayukanku (da kanku) yau zaa saka maku da walakantacciyar azaba, saboda abin da kuke fadi game da Allah da ba na gaskiya ba, kuma kun kasance kuna girman kai ga barin ayoyinsa.)

Hadisai mashahurai da dama sun zo a kan wannan zance, wajibi ne mumini yayi imani da kuk abinda Kur'ani da Hadisi suka zo da shi na game da wadannan boyayyun lamura, (wato gaibu). Kuma kada ya ki yarda da abin da zai auku na gaibu a cikin kabari wai don bai dace da abinda yake gani na yau da kullun ba. Ka sani cewa ba'a kamanta lamuran duniya da na lahira, don kuwa da akwai banbanci mai girman gaske tsakanin su, Allah dai ya taimaka.

## FASALI NA BIYAR

Muna kuma ba da gaskiya da kaddara, alherinta da na sharrinta. Wato ita kaddara ita ce abin da Allah Ta'ala ya kaddara a kan halitta, dan gane da yadda ya gabata a cikin iliminsa, da kuma ya tabbata a cikin hikimarsa.

Ita kaddara tana da matakai guda hudu.

**NA FARKO**

Shi ne sani; muna ba da gaskiya cewa lalle shi Allah Ta'ala masanin komai ne: ya san duk abin da ya kasance da wanda zai kasance, da kuma yanda zai kassance, duk wadannan suna cikin iliminsa na fil azal. Bubu wani abu da Allah ya jahilce shi, kuma Allah ba ya mantuwa:

**MATAKI NA BIYU:** Mun yi imani cewa lalle Allah Ta'ala ya rubuta a cikin: (LAUHUL MAHFUZ) ya rubuta duk wani abu da zai kasance, har zuwa ranar kiyama. Allah Ta'ala yace:

﴿أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۗ إِنَّ ذَٰلِكَ فِى كِتَٰبٍ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ﴾

(Ashe ba ka saniba, cewa: lalle Allah ya na sane da abin da ke cikin sama da kasa, lalle wannan yana cikin littafi, lalle wannan mai sauki ne a gun Allah).

**MATAKI NA UKU:** Nufi, wato muna ba da gaskiya cewa lalle shi Allah Ta'ala da nufinsa ne duk abubuwa da ke cikin sammai da kassai ke kasancewa. Babu wani abu da zai auku sai da nufinsa, abinda ya nufi afkuwarsa sai ya afku, in kuma bai nufa ba ba zai afku ba.

**MATAKI NA HUDU:** Halitta wato muna ba da gaskiya cewa lalle Allah Ta'ala

﴿ ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٞ ٦٢ لَّهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ ﴾

(shine ya halicci komai, kuma shine wakili a'kan komai. Duk taskan sammai da na kasa na sa ne).

Wadannan mata kai guda hudu da muka ambata, sun hade komai, wato duk wani abu da ya kasance daga Allah yake ko kuma daga bayinsa ne, fadi ne ko kuma aiki, ko kuma wani abin da ma sam baa iya an aikata shi ba, duk dai sanannu su ke a gun Allah, kuma suna nan a rubuce a guṇsa. Allah Ta'ala shi ne ya so afkuwar su kuma shi ne ya halicce su. Allah mai girma da daukaka yace:

﴿ لِمَن شَآءَ مِنكُمۡ أَن يَسۡتَقِيمَ ۞ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ﴾

(Ga wanda ya so daidaita a cikinku. (Kuma ba za ku so ba sai Allah Ubanjijin talikai ya so).

Ya kuma ce:

﴿ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقۡتَتَلُواْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَفۡعَلُ مَا يُرِيدُ ﴾

(in da Allah ya so, da ba su yaki juna ba. Amma Allah yana aikata abin da ya so). Ya kuma ce:

﴿ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَا فَعَلُوهُۖ فَذَرۡهُمۡ وَمَا يَفۡتَرُونَ ﴾

(In da Allah ya so da ba su aikata ba.) Sabili da haka rabu da su da abin da suke kagawa (na karya). Ya kuma ce:

﴿وَٱللَّهُ خَلَقَكُمْ وَمَا تَعْمَلُونَ﴾

(Allah shi ya halicce ku, da abin da kuke aikata wa).

Sai dai kuma muna imani cewa: lalle Allah Ta'ala ya bai wa bawansa zabi da kuma iko.

Muna da kwakkwaran dalilai da dama da ke nuna cewa duk wani aiki da dan Adam zai aikata, da sonsa ne kuma yana aikatawa da ikonsa ne.

Wadannan dalilai kuwa sune

**NA FARKO:** Fadin Allah Ta'ala da yayi cewa.

﴿فَأْتُوا حَرْثَكُمْ أَنَّىٰ شِئْتُمْ﴾

(Ku zo ma gonakinku yadda kuka so); abin nufi shine ku tara da matattakin ku ta inda kuka so. Da kuma fadinsa:

﴿وَلَوْ أَرَادُوا ٱلْخُرُوجَ لَأَعَدُّوا لَهُۥ عُدَّةً﴾

(In da sun so fita ne wallahi da sun yi masa tattali.) Ka ga a nan sai da Allah Ta'ala ya tabbatar cewa (mutum) zai iya zuwa in ya so kuma zai iya fita in ya bukaci yin haka.

**DALILI NA BIYU:** An ba wa dan Adam damar iya horon kansa (da aikata wasu abubuwa) ko kuma ya hana kansa aikata (wasu abubuwa) don kuwa inda mutum ba shi da zabi, ko kuma ba shi da iko cikin zartar da wasu lamura, da horo da ake yi, ya zama tilas, da mutum zai aikata abin da ba ya iyawa kenan, Yin haka kuwa ya saba wa hikimar Allah da kuma jinkansa, ya kuma saba wa fadin Allah Ta'ala na gaskiya da ya yi cikin Kurani cewa:

﴿ لَا يُكَلِّفُ اللَّهُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَا ﴾

Allah baya doro wa wata rai sai abin da za ta iya.

**DALILI NA UKU:** In da dai a ce aikin dan Adam ya kan afku ne ba da son sa ba ashe da sai muce yabo da Allah ya yi wa mai kyautata aiki wato (muhsini) da ya zama wargi da wasanni, kuma da azaba da za a yi wa masu sabo ta zama zalunci.

**DALILI NA HUDU:** Shine: cewa lalle Allah Ta'ala ya aiko manzanni, kamar yadda ya ce:

﴿ رُسُلًا مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى اللَّهِ حُجَّةٌ بَعْدَ الرُّسُلِ ﴾

(Masu bada bushara, kuma masu tsoratarwa. Don kada mutane su samu hujja (wani abin fadi) bisa ga Allah bayan manzanni). Da bawa ba ya aiki da ganin damarsa, da zabinsa, da hujjarsa a gaban Allah ba ta rushe ba.

**DALILI NA BIYAR:** Shine cewa: duk wani wanda zai aikata wani aiki, ya kan ji cewar ya aikata wani abu, ko kuma ya kan dena yin wani abin, ba da ya ji wani alama da ke nuni cewa yana kin yin haka ba. Misali shine cewa: mutum ya kan tashi ya tsaya, ko kuma ya zauna, kamar yanda ya kan kuma shiga ya kuma fita, ya kan kuma yi tafiya zuwa wata kasa. Kuma ya kan zauna bai yi tafiya ba. Duk wannan a kan ya so yin haka, kuma sam ba ya ji ko kadan cewa da wanda ke matsa masa yin haka. Ya kan ma iya tabbatarwa cewa aiki kaza ya aikata shi ne da sonsa ba da an tilasta masa ba. Haka ma shari'ar musulunci, ta rarrabe tsakanin wadannan lamura biyu wato abinda mutum ya aikata bisa sonsa, da abin da aka tilasta shi ya yi. A kan haka, Allah Ta'ala ba ya rikon mutum in ya aikata wani laifi da aka tilasta masa aikata shi ba da sonsa ba.

Muna yarda cewa lalle babu wani hanzari da mai sabon Allah zai iya gabatarwa a kan sabon sa, da sunan wai Allah ne ya kaddara. Dalili kuwa shine cewa: lalle shi mai sabon Allah ya kan afka ma sabon Allah ne da sonsa, kuma ba shi da ma tunanin cewa Allah ne ya kaddara masa yin wannan sabon, don kuwa ba'a iya gano kaddarar Allah sai bayan ta afku. Allah Ta'ala yace:

﴿وَمَا تَدْرِي نَفْسٌ مَّاذَا تَكْسِبُ غَدًا﴾

(Babu wani numfashi (wato rai) da ya san abin da zai aikata gobe). Ta kaka kuwa mutun zai kafa hujja da wani abu da ba shi da iliminsa, shine mutum ya aikata sabo sa'annan ya ce wai Allah ne ya kaddara.Irin wannan hujjar ba a aiki, don kuwa Allah Ta'ala na fadi cewa:

﴿سَيَقُولُ الَّذِينَ أَشْرَكُوا لَوْ شَاءَ اللَّهُ مَا أَشْرَكْنَا وَلَا آبَاؤُنَا وَلَا حَرَّمْنَا مِن شَيْءٍ
كَذَٰلِكَ كَذَّبَ الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ حَتَّىٰ ذَاقُوا بَأْسَنَا قُلْ هَلْ عِندَكُم مِّنْ
عِلْمٍ فَتُخْرِجُوهُ لَنَا إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا الظَّنَّ وَإِنْ أَنتُمْ إِلَّا تَخْرُصُونَ﴾

(Da sannu wadannan da suka hada Allah da bauta za su ce: Da Allah ya so ne, da ba mu yi shirka, ba, haka ma ubannemmu, da kuma ba mu haramta wani abu (da Allah bai haramta ba). Haka wadannan da suka zo gabanninsu suka karyata, har sai da suka dandani azabarmu. Ka ce: shin ko kuna da wani ilimi ne a kan haka, ai sai ku fito ku nuna shi. Babu abin da kuke bi sai zato, kuma karya kuke yi kawai.)

Kuma za mu iya ce wa shi wanda zai saba ma Allah, sa' annan ya ce mana wai Allah ne ya kaddara, za mu ce masa, mai ya hana ka gabatar da aikin kirki, kuma ka ce ai Allah ne ya kaddara. Don kuwa ai babu banbanci tsakanin

yin haka, tun da yake shi aikin kirkin ma ba wai ka san da zamansa ba ne gabannin afkuwarsa.

Sabili da haka ma, yayin da Manzon Allah ya fada wa sahabbansa cewa: lalle kowane daya a cikin ku an yi masa tattalin mazauni a cikin gidan aljanna, da kuma wani mazauni a cikin gidan wuta. Sai suka ce:in dai ya kasance haka, to mai zai hana mu dangana mu rabu da wani aiki? Sai Manzon Allah S.L.A.A.W.S. yace. A'a: Ku dai ku yi aiki, kowane daya zaa sawwake masa aikata abinda aka halicce shi don ya aikata. Wato in shi dan al'janna ne zaa sawwake masa aikata aikin 'yan aljanna, haka kuma in ya zama dan wuta.

Ga ma wani dan gajeren takadiri; da za mu ajiye ma shi wanda ke sabon Allah, kuma sai ya rika fadin cewa Allah ne ya kaddara, za mu iya ce masa kai dan uwa, mai kace in ya zamana cewa ka yi niyar tafiya zuwa Makka, sai ya kasance kuwa da akwai hanya biyu da ke sadar da mutum zuwa Makka. Sai ka samu wani amini mai gaskiya da ya sheda maka cewa: dayan wadannan hanyoyin ba ta da aminici, don kuwa tana cike ne da wasu abubuwa masu ban tsoro da firgita. Dayar kuma tana da aminci da saukin lamari. Sabili da haka sai ka bi hanya ta biyun ka bar ta farko, wai sai kace ai dama Allah ya kaddara hanyar da zaka bi, kai ba ka da zabi. Kaga a nan sai a lissafta ka cikin safun mahaukata.

Za mu iya ce masa kuma in misali an ajiye maka ayyuka biyu sai, ya zama dayan wadannan ayyukan biyu, ya fi

daya albashi mai tsoka, na san za ka dauki aiki mai albashi mai tsoka, in ko ya kasance haka, to mai zai sa ka zabar ma kanka kaskantaccen aiki a lahira, sa'annan ka ce wai Allah ne ya kaddara?

Za mu kuma ce ma mai sabon Allah mu kan ga in zazzabi ya kama ka, ka kan yawaita zuwa gidan likita, don jinyar kanka, kuma ka kan yi matukar hakuri da zafin ciwon aiki da zaa gudanar don fidda wannan cuta, kamar kuma yanda ka ke hakuri da dacin magani da kake dauka. To mai zai hana ka yi irin wanan hakuri a kan cuta da ke tare da zuciyarka na sabon Allah?

Muna ba da gaskiya cewa: har abada baa dangana wani sharri ga Allah Ta'ala don saboda cikakkiyar rahama da hikima da ke tare da shi Allah. Annabi mai tsira da aminci yace: sharri ba daga gare ka yake ba. (Muslim ne ya ruwaito). Shi dai hukuncin Allah har abada, ba za'a samu wani sharri a cikinsa ba, don kuwa yana fito wa ne daga rahamar sa da kuma hikimarsa.

Shi sharri dai a kan same shi ne a cikin abin da Allah ya hukumtar, don fadin Annabi S.L.A.W.S. da yayi a yayin da ya ke koya wa (jikansa) Alhasan R.L.A. yadda ake addu'ar kunutu, sai yace: (ka kiyaye ni daga sharrin abin da ka hukunta), ka ga a nan sai ya dangana sharri zuwa ga abinda shi Allah ya hukunta. Duk da haka kuma, shi sharri dai a cikin abinda Allah ya hukuntar, ba sharri ba ne tsantsa, wato dai zai iya zama sharri ta wata fuska, ya kuma zama alheri a wata fuskar daban.

Bala'i da kan auku a kan kasa na kamar fari, da cuta da talauci, da tsoro duk sharri ne, amma kuma zai iya zama alheri a wata fuskar. Allah Ta'ala yace:

﴿ ظَهَرَ ٱلْفَسَادُ فِى ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ بِمَا كَسَبَتْ أَيْدِى ٱلنَّاسِ لِيُذِيقَهُم بَعْضَ
ٱلَّذِى عَمِلُوا۟ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴾

(Barna ta bayyana fili, a cikin sarari da kuma teku, sabili da abin da hannayen mutane suka samar (na laifi) Allah zai dandana masu sashin abin da suka aikata, don su dawo (ga barin sabo).

Yanke hannun barawo ko kuma jefe mazinaci sharri ne a gun su. Amma kuma a wata fuskar alheri ne gare su, don kuwa yin haka zai zama masu kafara. Ka ga da haka ba za su sha azabar lahira ba. Har ila yau kuma alheri ne guda ta wata fuskar, don kuwa yin haka zai sa a kiyaye dukiyar mutane a kuma kiyaye mutunci, a kuma samu zuri'a masu asali, don kuwa yin haka zai hana yaduwar barna da fasikanci a cikin kasa.

## FASALI NA SHIDA

Ita wannan akida mai girma da daraja, wadda ke kunshe da irin wanan asali mai girma, tana haifar da diyar icce mai amfani, ga wanda yayi riko da ita.

## IMANI DA ALLAH DA SIFOFINSA

Ka ga imani da Allah Ta'ala, tare da sunayensa da sifofinsa, yana haifar da son Allah da kuma girmama shi a cikin zuciyar bawa, kuma wadannan abubuwa guda biyu (wato son Allah da girmama shi) sukan lizimta ma bawa bin umurnin Allah da kuma nisantar abubuwa da Allah ya yi hani ga barinsu, da kuma aikata abubuwa da Allah ya yi horo da yi, da kuma nisantar abinda ya yi hani ga barinsu. Da su ne akan samu cikakken dadin rai a nan duniya, da can lahira. Allah Ta'ala yace:

﴿ مَنْ عَمِلَ صَٰلِحًا مِّن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَنُحْيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةً طَيِّبَةً ۖ وَلَنَجْزِيَنَّهُمْ أَجْرَهُم بِأَحْسَنِ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴾

Wanda ya aikata aiki na gari, namiji ne ko mace, alhali yana mumini, wallahi za mu rayar da shi rayuwa mai kyau, kuma wallahi za mu saka masu ladansu da mafi kyawun abin da suka kasance suna aikata wa.

## AMFANIN IMANI DA MA LA'IKU

**NA FARKO:** Ya na sa mutum ya girmama Allah Ta'ala wannan da ya hallice su. Zai kuma san karfin Ubangiji, ya kuma san ikonsa.

**NA BIYU:** Ya na sa mutum ya rika godewa Allah sabili da matukar kulawa da shi Sarkin ke yi wa bayinsa. Don kuwa shine ya wakkala ma kowane daya a cikin bayinsa mala'iku biyu don su rika kiyaye su, suna kuma rubuta ayyukansu, da ma sauran wasu ayyuka da su ke zama amfani ne ga 'yan adam.

**NA UKU:** Ya na sa mutum ya so mala'ikun Allah, sabili da tsayuwarsu a kan bautar Allah Ta'ala cikin mafi cikakkiyar fuska, da kuma neman gafara da suke yi wa muminai.

## AMFANIN YIN IMANI DA LITTATTAFAN ALLAH

**NA FARKO:** Zai sa mutum ya san rahamar Allah, ya kuma san yawan kulawarsa da sha'anin bayinsa. Dalili kuwa shine Littafi da ya saukar wa kowace al'umma, don ya shiryar da su.

**NA BIYU:** Zai sa mu iya gane bayyanar hikimar Allah Ta'ala, cikin abubuwa da ya shar'anta wa kowace al'Umma, ta fuskar littattafai da suka dace da zamaninsu. Sai Ubangiji ya mai da karshen wadannan littattafai ya kasance shine Kur'ani mai girma, wanda ya dace da

halukan kowa, kamar yadda kuma ya dace da kowane zamani, kuma kowane bigire, har ya zuwa ranar kiyama.

**NA UKU:** Tabbatar da godiya ga ni'i'mar Allah Ta'ala da yayi mana na saukar da wannan littafi.

## AMFANIN IMANI DA MANZANNIN ALLAH

**NA FARKO:** Zai sa a san rahamar Allah Ta'ala, a kuma san yawan kulawarsa da lamarin halittarsa. Sabili da aiko Annabawa masu girma da daraja zuwa ga bayinsa, don su shiryar da mutane

**NA BIYU:** zai sa mutum ya gode wa Allah , a kan wannan ni'ima mai girma kuma mai yawa.

**NA UKU:** Zai kara wa mutum son wadannan Annabawan, ya kuma dada girmama su ya kuma kara yabon su, da irin yabo da ya dace da su. Don kuwa su ne Manzannin Allah, kuma su ne kebabbun bayinsa, da suka tsaya a kan bautarsa, da kuma isar da manzancinsa tare da yi wa bayin Allah nasiha, suka kuma yi matukar hakuri a bisa ga duk wani cuta da ta same su a cikin wannan aiki.

## AMFANIN YIN IMANI DA RANAR KARSHE

**NA FARKO:** Zai kwadaita wa mutum bautar Allah Ta'ala ta in da zai kaunaci ladan lahira, zai kuma sa mutum ya nisanci sabon Allah da tsoron azabar wanan rana.

**NA BIYU:** A cikin wannan rana ne mumini wanda ni'imar duniya da dadinta ta kubce masa, zai shakata da dadin ni'imar lahira, ya kuma ji dadin ladan aikinsa.

## AMFANIN IMANI DA KADDARA

**NA FARKO:** Ya na sa a samu kwanciyar hankali da hutun zucci. Don kuwa, duk lokacin da mutum ya sani cewa: duk abin da ya afku, hukunci ne na Allah , kuma duk wani abu hukuntacce ne daga Allah , babu shakka in ya yarda da haka, lalle zai samu kwanciyar hankali da natsuwar zuciya, ya kuma yarda da abin da Allah ya hukunta. Babu wanda ya kai mai imani da kaddara samun hutu da natsuwar zuciya.

**NA BIYU:** Samun natsuwar zuci da kwanciyar hankali, domin duk lokacin da ya san cewa abin ki ba ya samunsa sai da yardar Ubangiji da hukucinsa, ya kuma san cewa abin da Allah ya hukunta masa lallai sai ya same shi, to sai ransa ya natsu, ya rungumi kaddarar Allah, da sakankacewar zuciya. Babu mutumin da yake rayuwa mai

dadi a cikin kwanciyar hankali, kamar mai imani da kaddara.

**NA UKU:** Zai kore wa mutum duk wani ji-ji-da-kai inda duk wani abin alheri ko wata ni'ima ta same shi. Sai ka ga ya gode wa Allah Ta'ala, kuma ba zai yi mamaki da kansa ba cewa dabararsa ce ko kuma iliminsa ne.

**NA HUDU:** Zai kore wa mutum duk wani bacin rai ko kuma in bai sami biyan wata bukata ba, ko kuma in ya na cikin wani tsanani. Don kuwa ya yi Imani cewar haka ba zai faru ba sai da hukuncin Allah Ta'ala, Sarkinnan da ke mallakar sammai da kasa. Kuma babu abin da mutum zai yi sai kawai ya yi hakuri da abinda ya afku, in kuwa ya yi hakuri zai samu ladan hakurinsa. Wannan shine manufar Allah Ta'ala a cikin littafinsa mai girma da yake fadi cewa:

﴿مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ فِي ٱلْأَرْضِ وَلَا فِيٓ أَنفُسِكُمْ إِلَّا فِي كِتَٰبٍ مِّن قَبْلِ
أَن نَّبْرَأَهَآ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ﴿٢٢﴾ لِّكَيْلَا تَأْسَوْا۟ عَلَىٰ مَا فَاتَكُمْ وَلَا
تَفْرَحُوا۟ بِمَآ ءَاتَىٰكُمْ ۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ﴾

(Wata musiba ba ta taba samuwa ba, ko a ban kasa ko kuma cikin kawunanku, face duk yana cikin littafi (lauhul mahfuz) kafin mu halicce ta (wato ita wannan kasar da ita wannan ran) lalle wannan abu ne mai sauki ga Allah.

Domin kada ku bata ranku da abin da ya kubce maku kuma kar ku yi fariya da abin da (Allah) ya ba ku, Allah ba ya son duk mai yawan takama mai yawan al-fahari).

Allah Ta'ala muke roko ya tabbatar da mu a kan wannan akida, ya kuma sa mu dace da amfaninta, ya kuma dada mana fallalar nan tasa,kuma kada ya karkatar da zukatanmu bayan ya shiryar da mu, ya kuma yi mana baiwar jinkai daga gunsa.

Lalle shi ne (sarki) mai baiwa. Godiya kuma ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da amincin Allah kuma su tabbata ga Manzonsa Annabi Muhammadu, tare da jama'ar gidansa, da sahabbansa da mabiyansu a cikin kyautata aiki.

## TAMMAT DA TAIMAKON ALLAH

## NA GAMA TARJAMA WANNAN LITTAFI

## SAFIYAR LARABA

## DA TA DACE DA RANA TA TA MILADI

Da godiyar Allah mai girma da daukaka, Allah nike roka ya sa albarka a cikin wannan littafi, ya kuma amfanar da dukkan al'umma da shi, amin summa amin.

SHU'AIB ABUBAKAR UMAR
POST OFFICE BOX 229
NIMA, ACCRA, GHANA, WEST AFRICA.

مطابع الناشر العربي
AL-NASHER AL-ARABI P. PRESS

# عقيدة أهل السنة والجماعة

تأليف

الشيخ محمد بن صالح العثيمين

باللغة الهوسا

وكالة المطبوعات والبحث العلمي
وزارة الشؤون الإسلامية والأوقاف والدعوة والإرشاد
المملكة العربية السعودية

١٤٣٥ هـ